# Daga Abdullahi Dan Abbas-Allah ya yarda da shi- ya ce Manzon Allah-tsira da Amincin Allah su tabbata a gareshi ya ce game da 'Diyar Hamza: "Bata halatta a gare ni ba, domin shayarwa ta haramta abin da nasaba take haramtawa, kuma ita Diyar Dan uwana na shayarwa ne

Daga Abdullahi Dan Abbas-Allah ya yarda da shi- ya ce Manzon Allah-tsira da Amincin Allah su tabbata a gareshi ya ce game da 'Diyar Hamza: "Bata halatta a gare ni ba, domin shayarwa ta haramta abin da nasaba take haramtawa, kuma ita Diyar Dan uwana na shayarwa ne

[Ingantacce ne] [Bukhari da Muslim suka Rawaito shi]

Aliyu Dan Abu Dalib-Allah ya yarda da shi- daga Annabi cewa ya Auri 'Diyar Baffansa Hamza. sai ya bashi labari cewa bata halatta a gareshi ba, domin ita 'Diyar Dan uwansa ce da aka shayar da su tare, kuma cewa shi da Baffan sa dukkansu Suwaiba ta shayar da su kuma baiwa ce ta Abu Laha, sai ya zamanto Dan uwansa ta wajen Shayarwa, kuma ya zamanto Baffan 'Diyarsa, kuma ya haramta ta hanyar shayarwa, duk abunda haihuwa ta haramta.

https://sunnah.global/hadeeth/ha/show/6162